# Tsara ayyukan al'ummarku

Takardar aikin da ke ƙasa an samo ta ne daga (***Matasa da masu tsattsauran ra'ayi***).[1] bayanai domin amfanin matasa ma'aikata. Ku yi nazarin tambayoyi da ke ƙasa sannan ku rubuta amsoshinku a kan takarda. Za ku iya zayyano abin da kuka ɗauka a matsayin al'ummarku, tare da barin wadataccen fili a ciki da wajen farfajiyar domin rubuta amsoshinku.

## A CIKIN AL'UMMAR

Mataki na farko shi ne a fahimci mene ne ya haɗu ya samar da al'ummarsu, sannan a zarce zuwa tambayoyin da ke kasa.

- A ina muhimman alamomin ƙasar suke? Waɗanne wurare ne ake da su (wuraren ibada, makarantu, da sauransu)?
- Waɗanne nau'ukan kasuwance ne ke cikin al'ummar sannan a wane wuri suke? Waɗanne ƙungiyoyin matasa, ko kula kulob-kulob na al'umma ne ake da su? Ku sanya dukkannin waɗannan a kan taswirarku.
- Waɗanne nau'ukan mutane ne ake da su a cikin al'ummar? Shin sun mamaye wani wuri takamaimai ne? Ta yaya suke yawo a cikin al'ummar? Ina matasa da ke cikin al'ummar? Wane wuri ne aka samar musu?
- Waɗanne shirye-shiryen matasa, ƙirkire-ƙirkire, da damarmaki ne ake da su? A ina? Wane wuri ne yake da aminci, ko yake da haɗari ko yake buɗe sannan yake da aminci ga matasa a waɗansu lokuta kawai na rana.
- Wane wuri ne matasa ba za su iya zuwa ba?
- A ina ne ake samun rikici? Ina ne matasa za su iya zuwa domin samun kariya ku su ji cewa suna cikin aminci?
- Yaya wannan wuri yake komawa da dare?
- Ta yaya wurin ke sauyawa a waɗansu lokutan shekara, ko yayin gudanar da waɗansu al'amura ko kuma yayin da waɗansu abubuwa suka auku?

## A WAJEN MUHALLIN AL'UMMA

- Waɗanne barazana al'ummar ke fuskanta? Daga ina waɗannan barazana ke tasowa?
- Waɗannan mutane ne ba 'yan cikin gida ba da ke yawan zuwa muhallin al'ummar? Daga ina suke zuwa? Me ya sa?
- Wa ke yanke hukunci game da yadda muhallin al'ummarku zai kasance? A bisa wane dalili?
- Waɗanne sauye-sauye ne za su iya yin tasiri a kan fasalinta da iyakokinta a nan gaba?

## KWANKWANCE AL'UMMARKU

Yi tunani game da taswirar al'ummarku daidai da fahimtarku:

- Waɗanne wurare ne kuka fi zuwa? Me ya sa kuke son zuwa wuraren?
- Waɗanne wurare ne ke da aminci a gare ku yayin ziyara? Waɗanne ne ba su da shi?
- Shin za ku iya zuwa waɗansu daga cikin wuraren tare da waɗansu mutane? Wa?
- Me ya kamata ku fara nema yayin da kuka shiga waɗannan wurare?
- Wane irin sauyi aka samu a waɗannan wurare bayan lokaci?

## AMFANI DA NAZARINKU

Ku yi la'akari da tambayoyin da ke sama:

- Ta wace hanyar bayanan da kuka tara sannan kuka zayyano za su samar da amsa ga tambayoyin?
- Waɗanne tambayoyi ne bayanan ba su samar da amsoshinsu ba? Me ya sa?
- Waɗanne sababbin tambayoyi ne suka taso?

---

1. Copyright: SALTO Cultural Diversity Resource Centre, 2016 www.salto-youth.net/diversity Reproduction and use for non-commercial purposes are permitted provided the source SALTO Cultural Diversity Resource Centre www.salto-youth.net/diversity is mentioned and diversity@salto-youth.net is notified. The project has been funded with support from the European Commission. This publication reflects the views only of the authors. The European Commission and the British Council cannot be held responsible for any use which may be made of the information contained within.